“Duk macen da ta yi aure ba tare da izinin waliyinta ba, to aurenta ɓatacce ne - sau uku - idan ya tare da ita, to sadakin ya kasance nata ne saboda abinda ya samu na (jima'i) daga gareta, idan suka yi jayayya to sarki (shi ne) waliyyin wanda ba shi da waliyyi

Daga Nana Aisha Uwar muminai - Allah Ya yarda da ita - ta ce: Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya ce: “Duk macen da ta yi aure ba tare da izinin waliyinta ba, to aurenta ɓatacce ne - sau uku - idan ya tare da ita, to sadakin ya kasance nata ne saboda abinda ya samu na (jima'i) daga gareta, idan suka yi jayayya to sarki (shi ne) waliyyin wanda ba shi da waliyyi".

[Ingantacce ne] [Abu Dawud da Tirmizi da Ibnu Majah da Ahmad ne Suka Rawaito shi]

Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya tsoratar da mace ta aurar da kanta ba tare da izinin waliyyanta ba, kuma cewa auranta ɓatacce ne, haƙiƙa ya maimaita hakan sau uku, kamar ka ce bai kasance ba. Idan wanda ya aureta ya tare da ita ba tare da izinin waliyyinta ba; to sadaki cikakke nata ne saboda abinda ya samu na jima'i da ita a farjinta. Sannan idan waliyyan suka yi jayayya a cikin waliccin ɗaura auren - kuma darajojinsu a cikinsa ɗaya ne - to ɗaura auren ga wanda ya riga zuwa gare shi ne daga cikinsu idan a hakan akwai duba maslaha daga gare shi, idan waliyyi ya hanu daga aurarwa to kamar ba ta da waliyyi ne; sai shugaba ko wakilinsa cikin alƙalai da wasunsu su zama waliyyanta, inba haka ba to babu walicci ga sarki tare da samuwar waliyyi.

http://www.sunnah.global/hadeeth/ha/show/58067